Ni nasan in kina farin ciki dani, kuma haka idan kina fushi da ni

An karvo -Allah ya yarda da ita- ta ce: Manzon Allah SAW ya ce: "Ni nasan in kina farin ciki dani, kuma haka idan kina fushi da ni" sai ta ce: sai na ce: ta yaya kake gane hakan ? sai ya ce: "Idan kina farin ciki sai kice a'a na rantse da Muhammad kuma idan kina fushi da ni sai ki ce na Rantse da ubangijin Ibrahim" sai ta ce: na ce: Ey wallahi haka ne ya Manzon Allah, bana qauracewa sai sunanka

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Nana Aisha -Allah ya yarda da ita- ta ce: Manzon Allah SAW ya ce da ni: "Lallai ni ne mafi sanin lokacon da bakya fushi da ni, da kuma lokacin da kike fushin da ni, sai ta ce da shi: ta yaya ka sani hakan? sa i Manzon Allah SAW ya ce: "idan kina fushi da ni awani kina cewa: Na rantse da Ubangijin Muhammadu, sai ki kirawo sunana a cikin rantsuwarki, kuma idan kina fushi da ni akan wani abu na duniya da yake da alakar zamantakewar Aure, sai ki ce a cikin rantsuwarki: na rantse da Ubangijin Ibrahim, sai ki kaucewa faxar suna na zuwa sunan Ibrahim sai ta ce: E haka ne Wallahi ya Manzon Allah, ba zan bari ba sai faxar sunanka akan Harshena tsawon fushi na, sai dai Soyayyarka tana nan daram cikin Zuciyata

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/11180